# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Aljannar Kare – Haɗarin afkawa cikin bashi
## Kashi na biyu: Illar rayuwa cikin bashi


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | James Muhando |
| Wanda ya fassara: | Danlami Bala Gwammaja |
| Wadda ta tace: | Halima C. Schmaling |


**'Yan wasa:**

| | |
|---|---|
| Mai ba da labari: | ɗan shekara 30 |
| Malama Rabi: | 'yar shekara 30 |
| Ali: | ɗan shekara 15 |
| Jamila: | 'yar shekara 15 |
| A'i: | 'yar shekara 16 |
| Bash: | ɗan shekara 15 |
| Binta: | 'yar shekara 11 |
| Nana: | 'yar shekara 35 |
| Lawan: | ɗan shekara 40 |
| Zaliha: | 'yar shekara 35 |
| Kawu Natanko: | ɗan shekara 45 |
| Hajjia Larai: | 'yar shekara 55 |

**Mai ba da labari:**

Masu saurarenmu, barkanmu da sake saduwa a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu”. Ina fatan za ku ɗan yi min afuwa saboda kun riske ni ina cin abincin rana. Ga waɗanda wannan ita ce saduwarmu ta farko, to ni dai sunana Aliyu Bello, kuma ni ne jam’I mai ba da bashi a wannan gari, kuma ni ne jagoran wannan shiri mai taken “Aljannar kare – Haɗarin afkawa cikin bashi” wanda shiri ne a kan matsalolin da ke tattare da cin bashi.

Idan ba ku manta ba ina ba ku labari ne a kan yadda rayuwata ta kasance a lokacin da nake makaranta, da kuma irin sakarkarun abokan da nake da su. Ajinmu yana ɗaya daga cikin irin ajujuwan da duk wani yaro ɗan shekara 15 zai so a saka shi domin kuwa cike yake da hayaniya, ga ba’a, ga kuma barkwanci! A wannan safiya da nake ba ku labari mun tashi kamar yadda muka saba cike da barkwanci.

**Fitowa ta 1: A makaranta**

**Ɗalibi 1:** Kun san kuwa saboda tsananin tsawon baban Iro ba ya iya wucewa ta cikin ƙofa sai ya durƙusa.

**Ɗalibi 2:** Kai kuma naka baban saboda tsananin gajartarsa ba sai ya yi kwanto a ƙasa ba don kauce wa harsashi idan ya ji ana harbe-harbe.

**Ɗalibi 3:** Kai kuma saboda tsananin baƙinka sai kana ce wa mutane ihu, ku kauce idan za ka wuce saboda ba sa ganinka!

**Malama Rabi:** Barkanku dai! Ina kwananku? An dawo hutu ƙalau? To, kowa da kowa ya natsu! … To madalla. Na san dai kowa ya ji daɗin hutun da aka yi. Yanzu kowa ya buɗe shafi na …

**A’i:** Kowa da kowa amma ban da Bash.

**Malama Rabi:** Ke A'i, ban ce idan ina magana ki daina sa baki ba! Me ya sa idan kina da magana ba za ki ɗaga hannunki ba? Shi ke nan. Akwai wanda yake so ya ce wani abu? ... To, A'i na ga kina ɗaga hannu, me za ki ce?

**A'i:** Malama Rabi, Bash fa ba ya zuwa makaranta.

**Malama Rabi:** To na ji. Shin akwai wanda ya san dalilin da ya sa ba ya zuwa? ... Kai fa Ali?

**Ali:** Gaskiya Malama, ban sani ba.

**Malama Rabi:** Jamila fa?

**Jamila:** Wallahi, ni ma ban sani ba, Malama.

**Malama Rabi:** To shi ke nan. Yanzu ku biyun nan na ba ku aiki. Idan kun koma gida ku binciko mana dalilin da ya sa ba ya zuwa. Shi ke nan, mu ci gaba…

**Mai ba da labari:**
Sai dai kuma abin da Malama Rabi da ma mu masu sauraro ba mu sani ba shi ne, mu mun ɗauka cewa yanzu haka Bash yana can a gida ne a kwance saboda ba shi da lafiya, amma abin ba hake yake ba. Ga Bash can yana ta tunanin yadda zai yi ya biya kuɗin keken nan da ya karɓo bashi. Allah Sarki, shi dai Bash ba ya son zuwa makaranta ne saboda ba ya son ya fuskanci tsokanar abokansa, saboda asarar sabon kekensa da ya yi.

**Fitowa ta 2: A gidan su Ali**

**Bash:** Ksss, Ali! Ali! Ni ne fa Ali, don Allah buɗe min in shigo.

**Ali:** Kai kuwa Bash, me yake tafe da kai cikin wannan daren?

**Bash:** Shhh! Ka dinga magana a hankali mana. Buɗe min in na shigo na yi maka bayani.

**Ali:** Shi ke nan, bari na buɗe maka ƙofa.

**Bash:** A’a, tsaya! Kar ka buɗe mini. Bari dai na shigo ta wundo. Ba na son babarka ta san na zo nan gidan.

**Ali:** Shi ke nan Bash. Miƙo min hannunka na janyo ka ta tagar. Kama!

**Bash:** Riƙe mini da kyau! … Yauwa, har na ɗan ji daɗi. Kai, amma fa a waje akwai sanyi!

**Ali:** To gaya min, Bash, me yake faruwa? Yaya aka yi na gan ka cikin kayan makaranta, kuma na san ko makaranta ba ka je ba ma.

**Bash:** Ni yanzu na zo ne ka taimaka min na kwana a nan tun da dare ya yi, ka san ba zan iya zuwa gida na kwana ba, Da safe sai na wuce gida.

**Ali:** To, na ji. Amma dai bai kamata ka ɓoye min komai ba, ni fa abokinka ne!

**Binta:** Ali! Kai Ali! Da kai da wa na ji kuna magana?

**Ali:** Yi maza ka ɓuya a ƙarƙashin gado! … Ke Binta, kar ki kuskara ki shigo min ɗaki, karatu zan yi!

**Binta:** Yau ga Ali yana magana shi kaɗai. …

**Mai ba da labari:**

Da dai Bash ya ji Binta ta kauce ba ta shigo ɗakin ba, sai ya yi ajiyar zuciya. Yanzu kam zai iya yin barci, in ya so gobe ya ci gaba da ji da matsalar da take damunsa. Amma kuma da yake ƙaddara ta riga fata, matsalolin nasa ba su lafa ba a wannan daren!

**Fitowa ta 3: A gidan su Bash**

**Nana:** Tabbas wannan Bash ne. Ya kamata kuwa a ce yana da ƙwaƙwaran dalilin da ya sa ya yi dare! … Bash, ka san kuwa yanzu ƙarfe nawa ne? ... Ashe Maigida ne. Yi haƙuri, na ɗauka Bash ne.

**Lawan:** Bash kuma? Ban gane ba? Kar dai ki ce min har yanzu bai dawo gida ba?

**Nana:** Bai dawo ba kam. Ni na ɗauka kuna tare. Shi ne ma ya sa ban neme shi ba. … To shi kuwa ina ya je? Yanzu fa kusan ƙarfe goma!

**Lawan:** Kin ga, zo mu shiga ciki mu jira shi.

**Nana:** Yanzu don Allah a ce ɗan nan bai dawo gida ba, amma kawai ka ce, “zo mu shiga ciki mu jira shi”?!

**Lawan:** Don Allah ki daina damuwa! Ɗanki fa ya riga ya yi girma. Mu jira shi nan da rabin awa, idan bai zo ba sai mu fita mu neme shi.

**Nana:** To, ba kome, mu shiga!

**Mai ba da labari:**
Sai dai kuma har bayan awa guda suna jira, amma Bash bai dawo gida ba don haka suka fita nemansa. Daga nan kuma sai suka nufo gidanmu. A lokacin da suka zo mun riga mun yi barci, amma ƙarar ƙwanƙwasa ƙofar da suka yi sai ta tashe mu.

**Fitowa ta 4: A gidan su Ali**

**Nana:** Salamu alaikum.

**Zaliha:** Wane ne?

**Nana:** Buɗe mana, Zaliha. Ni ce Nana.

**Zaliha:** Nana kuma!? … Shigo mana, Nana. Ashe har da Malam Lawan kuke tafe. Ku kuwa me kuka zo nema cikin dare haka? Lafiya?

**Lawan:** Muna neman yaron nan ne, Bash. Ko kun gan shi ya zo gidan nan?

**Zaliha:** Bash? Anya kuwa? Amma dai bari in tambayi Ali. … Ali! Kai Aliyu! … Ko ka ga abokinka Bash? Ga iyayensa nan sun zo nemansa!

**Ali:** Kai Bash! Kai Bash! Tashi ga iyayenka sun zo! Kai Bash, tashi!

**Zaliha:** Me nake ji haka?

**Ali:** Ba komai, Mama!

**Zaliha:** Kai Aliyu. Ba da kai nake magana ba ne? Ina tambayarka ko ka ga Bash? Ko kuwa sai na shigo cikin ɗaki na same ka?

**Ali:** Ba haka ba ne, Mama. Wallahi ban gan shi ba! … Yi maza, yi maza ka fita kafin ta shigo!

**Bash:** To, yanzu ina za ni cikin wannan daren?

**Ali:** Ni ma ban sani ba. Yi maza ka riga su zuwa gida kuma ka gaya musu a makaranta ka tsaya, ko kuma mu kawo musu wani dalili!

**Bash:** To me zai hana na tsaya na ɓuya a ƙarƙashin gadonka?

**Ali:** A'a, ni fa na san babata. Ba inda ba za ta duba ba. Duk sai ta bincike ɗakin nan! Malam kai dai kawai ka tafi!

**Zaliha:** Kai da wa kuke magana ne, Aliyu?

**Ali:** Ba kowa, Mama.

**Zaliha:** Anya kuwa ba kowa a ɗakin nan naka? Bari in duba!

**Ali:** Tsaya mana, Mama! Ai ba sai kin bincike ɗakin ba. Wallahi ba kowa a ciki.

**Zaliha:** An ce maka iyayen Bash ne suka zo suna nemansa, ko ka gan shi bayan da aka taso daga makaranta yau?

**Ali:** A'a, ni ban gan shi ba, Mama.

**Mai ba da labari:**

Daga nan dai sai iyayen Bash suka gaji da nema suka koma gida. Amma abin mamaki, da suka koma gida sai suka ga ɗan nasu a dunƙule a kan gado. Kuma ya ce musu ya tsaya yana karatu ne a makaranta bai ma san dare ya yi haka ba.

To, da yake ina ba ku labari ne a kan irin bahagwayen mutanen nan, sai na tuna ashe ban taɓa ba ku labarin wani kawuna mai suna Natanko ba. Shi dai kawu Natanko mutum ne mai azama tun yana ƙaraminsa kamar yadda babata ta shaida mini. Shi mutum ne mai son jin daɗi. Ya kan zaɓi wurin zama mafi kyau. Ba abin da yake sai cin bashi, a ƙarshe ma dai ya ɓige da zama ɗan caca, sannan ya dinga yi wa abokansa da masu binsa bashi ƙarya. Shi dai kawuna ya kasanace faƙiri ne, kuma yana zaune ne a wani ɗan tsukukun gidan haya mai ɗaki ɗaya. Amma kuma sai ya dinga nuna wa mutane cewa, shi fa harkar fulotai yake yi da gine-gine.

**Fitowa ta 5: A cikin gari**

**Mai gidan haya:** Natanko! Kai Natanko, buɗe ƙofa na ce! Na san kana ciki. Ka buɗe na ce! Na ji lokacin da ka shigo ta wundo, sai ka ce ɓarawo. Ka buɗe mana! …

To shi ke nan! Tun da abin haka yake, ba ni da wani zaɓi illa na gaya wa ɗana ya zo ya ɓalle ƙofar! Kuma kar ma ka fara tunanin za ka fice ta wundo domin ɗayan ɗan nawa yana nan a tsaye a waje!

**Natanko:** Hajiya, don Allah ki yi haƙuri! Wallahi barci nake mai nauyi! … Kai, amma dai shigarki ta yi kyau yau!

**Mai gidan haya:** Kai fa ka ɗauke wata wawiya ko? To ga wawiyar taka nan ta zo karɓar kuɗin hayarta. Yanzu-yanzun nan kuwa!

**Natanko:** Ayya Hajiya, ai ba wata matsala. Ni har ma na sauran watannin zan biya ki duka.

**Mai gidan haya:** Kai ɗin ne za ka biya ni har na sauran watannin? Ka gaya wa wata ba ni ba!

**Natanko:** Gaskiya nake gaya miki, Hajiya Larai! Wato ina sa ran wasu cak ɗin kuɗi ne masu yawa. Kuma nan da sati biyu za su samu.

**Mai gidan haya:** Amma ka tuna da abin da ka gaya min watan da ya shige?

**Natanko:** Na tuna mana, wato wata 'yar matsala aka samu daga ɗaya daga cikin masu sa hannu cak ɗin. Amma yanzu komai ya daidaita, kar ki damu.

**Mai gidan haya:** Ba za ta saɓu ba! Ka daɗe kana raina min hankali, kuma ni yanzu na gaji! Ka kwashe ya-naka-ya-naka ka bar mini gidana kawai!

**Natanko:** Allah Sarki, Hajiya. Don Allah ki bar ni na kwana zuwa gobe da safe, sai na kwashe kayan nawa na bar miki gidan!

**Mai gidan haya:** Wato don ka samu ka sake yi min wata ƙaryar da safe ko? To ban yarda ba!

**Natanko:** To, ni kuwa ina za ni a wannan tsohon dare, Hajiya?

**Mai gidan haya:** Ba abin da ya sha min kai. Ni dai ka fice ka bar min gidana!

**Natanko:** Don Allah Hajiya, ki taimaka min, Hajiya!

**Mai gidan haya:** Ka fice min daga gida na ce!

**Natanko:** To bari in kwashe kayan nawa.

**Mai gidan haya:** Ni ban yarda ba. Ba inda za ka kwashe kayanka ka tafi ba sai ka biya ni kuɗina. Kauce ma in kulle ƙofar!

**Natanko:** Don Allah Hajiya, don Allah ki yi haƙuri! …

**Mai ba da labari:**

Masu saurarenmu, yanzu bari na garzaya na koma ofis kafin shugabata ta fara ciccika tana kumbura. Amma idan kuna son ku sake sauraron wannan shiri, za ku iya ziyartar shafinmu na yanar gizo a dw.de/lbe. Kuma za ku iya tuntuɓarmu a shafinmu na 'Facebook'. Kafin nan sai na ce muku mu jima da yawa!